


An yi wani mutum.

Sunansa Keri.



Keri yana da

agwagwa.

Agwagwa tana yin


ƙwai ɗaya.

Keri kan sayar da

ƙwai ɗaya.

Yana samun kuɗi

kowace rana.





Keri bai gode wa


Allah ba.

Ya raina abin da yake


samu.

Keri yana son ƙwai da yawa.

Yana son kuɗi da yawa.







Keri ya yanka

agwagwa.

Yana son dukkan ƙwan

cikin agwagwa.



Keri ya sami ƙwai

ɗaya.

Kwan ma bai riƙa ba.



Keri ya tashi a tutar babu.

Ba shi ga ƙwai.

Ba shi ga agwagwa.